# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na biyu: Fafutukar neman daidaito – Lois Auta daga Najeriya

Wadda ta rubuta: Katrin Gänsler
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

Mai ba da labari
Lois Auta: ’yar shekara 31
Mathilda Auta: ’yar shekara 20
Sergio Mainetti: ɗan shekara 44
Jamilah Hamza: ’yar shekara 45

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na biyu na shirinmu na "Ji Ka Karu" mai suna "Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi – Mutunta Haƙƙin Tsirarru". A cikin wannan shirin za mu ji bayanin wasu tsirarrun mutane ne waɗanda a saboda waɗansu dalilai na dabam ake nuna musu bambanci a rayuwarsu ta yau da kullum. Misalin da za mu bayar shi ne, kamar na mutanen da suke da wata nakasa a jikinsu. A shirin namu na yau za mu kai ziyara ne Tarayyar Najeriya, inda za mu gana da wata mata mai suna Lois Auta. Ita dai wannan mata 'yar shekara 31 tana zaune ne a wani ɗan ƙaramin gida a babban birnin Tarayyar Najeriya, wato Abuja. A kullum sai wani ya zo ya taimaka mata saboda tun tana 'yar shekara biyu ba ta iya tafiya sai an tura ta a kan keken guragu. Sai dai kuma duk da wannan nakasa da take da ita, Lois tana ci gaba da rayuwarta kamar yadda ta saba, don haka ne ma take son ta ƙarfafa wa sauran mutane da suke da nakasa gwiwa don su ma su ci gaba da rayuwarsu kamar kowa.

**Mai ba da labari:**

Yanzu dai ga direban wannan mata nan Isaak, ya ɗauko keken guragun nan daga bayan mota mai launin azurfa. Nan take ya haɗa shi domin Lois Auta ta samu ta zauna a kai. Lois dai tana jin daɗin irin taimakon da wannan direba nata mai haƙuri yake yi mata. Da ba don irin wannan taimakawa da yake yi mata ba da wannan mata 'yar shekara 31 ba ta samu damar yin aiki ba. Duk da cewa ta ƙoƙarta ta yi mai wuyar, wato ta hau kan wannan keken guragun, amma sai da ta ɗauki tsawon minti 20 kafin ta kai ga katafaren ofishin nan na Ma'aikatar Man Fetur ta Najeriya.

Ga dai Lois nan a kan kekenta na guragu tana ƙoƙarin bi ta hanyar da akan yi wa mutane nakasassu irinta. Ga shi kuma ana zafi, dole sai wannan matashiya tana yi tana jan birki tana hutawa, kuma tana share gumi daga fuskarta. A ƙarshe dai, yanzu ta samu ta kai ga ƙofar nata ofishin. Ga dai Lois nan baki har kunne, duk kuwa da jidalin da ta sha.

**Bayanin Lois:**

*“Ina yawona ko’ina ba tare da na nemi mutane su taimaka mini ba domin kuwa babu inda ba a yi magangari ba. An yi shi ne domin mutane nakasassu su dinga bi. Shi ya sa ma ofishina ya dace ƙwarai da mutanen da suke da wata nakasa. Lallai ana tunawa da mu, kuma ana matuƙar ba mu kulawa mai kyau.”*

**Mai ba da labari:**

Wannan yanayi na kulawa dai ba kasafai ake samunsa a cikin ƙasa ta Najeriya ba. Daga cikin fiye da mutane miliyan 150 da ke zaune a wannan katafariyar ƙasa, an ƙiyasta cewa akwai kusan mutane miliyan 20 zuwa 22 da ke da wata nakasa ta jiki. Amma duk da wannan yawa nasu an mayar da su saniyar ware a cikin harkokin rayuwa na yau da kullum. Malama Jamilah Hamza ta yi bayanin irin matsalolin rayuwar da nakasassu ke fuskanta a kullum. Malama Jamilah Hamza dai tana aiki ne a Hukumar Kare Haƙƙin Ɗan Adam. Ita ce jami’ar kula da matsalolin nakasassu.

**Bayanin Jamilah:**

*“Yawancin gine-gine da kuma ofisoshin gwamnati ba sa shiguwa ta daɗi ga mutane nakassu. Sai ka ga an yi gini, amma an ƙi yi masa magangari, ko kuma an ƙi sa masa lifta. Yanzu ka ga ke nan idan mutum yana da wata nakasa, ko a kan keken guragu, ko kuma yana dogarawa da sanda, idan yana son ya kai ga wani wuri misali a hawa na biyar ga shi kuma babu magangari ba lifta, to fa ba shi da damar kaiwa ga wannan wuri. Don haka ko ma me yake so za a yi masa a wannan ofishin, yanzu ke nan ba zai samu ba, tun da ba zai iya kaiwa ga wurin ba.”*

**Mai ba da labari:**

Najeriya dai ta rattaba hannu a kan ƙudurin Majalisar Ɗinkin Duniya a kan Haƙƙin Mutane Nakassu tun cikin watan Disambar shekara ta 2010. Fatan da ake da shi na yin wannan doka shi ne, don a kawar da matsalar da nakasassu suke fuskanta ta fuskar harkokin yau da kullum da kuma harkokin shari’a a duk faɗin duniya. Sai dai kuma a ƙasar ta Najeriya babu abin da ya sauya tun

daga lokacin da ta sa hannu a kan wannan ƙuduri. Waɗanda wannan ƙuduri ya shafa na ta zuba ido su ga gwamnatin Najeriya ta fito da wata sabuwar doka wadda za ta ƙunshi tanade-tanaden da aka yi a cikin wancan ƙuduri na Majalisar Ɗinkin Duniya. Bayanin da muka samu a lokacin da muka ziyarci ofishin Malama Jamilah Hamza shi ne cewa, dokar da majalisar ƙasar ta yi a shekara ta 2011 a kan wannan batu, har yanzu tana nan a gaban shugaban ƙasa Goodluck Jonathan, tana jiran sa-hannunsa. Sai fa idan shugaban ya sa hannu ne, mutane nakasassu za su samu hujjar neman haƙƙinsu da kuma ƙalubalantar gwamnati. Malama Jamilah Hamza ta ƙagara hakan ya faru.

**Bayanin Jamilah:**

*"Da zarar shugaban ƙasa ya sa hannu a wannan doka, za a fadaɗa haƙƙin nan na samun ilimi ga mutane nakasassu, da na kiwon lafiya, da na samun damar shiga ofisoshi da gine-gine, da na samun bayanai. Wataƙila a duk tashoshin gidajen talabijin ɗinmu za mu samu masu yin tafinta da hannu a lokacin da ake karanta labarai. Aikin waɗannan masu yin tafinta shi ne, su dinga fassara wa kurame abubuwan da ake faɗa."*

**Mai ba da labari:**

Yanzu ga Lois nan tana zaune a kan kujerarta tana tafa wasu wasiƙu a cikin komfuta. Ita dai tana aikin sakatariya ne a Kamfanin Man Fetur na Najeriya, wato NNPC. Kuma alhakinta shi ne kula da ababan hawa na kamfanin. Alal misali, alhakinta ne ta tabbatar da cewa ana kula da motocin kamfanin a ko da yaushe. Yanwanci tana yin wannan aikin ne tare da wasu abokan aikinta su huɗu. Sai dai kuma yau duk ba sa nan sai ita kaɗai. A lokacin da take kammala rubuta wannan wasiƙa, Lois ta tuno lokacin da ta fara cutar da ta yi sanadiyyar wannan nakasa tata.

**Bayanin Lois:**

*"Bayan da aka yi mini bikin cika shekaru biyu da haihuwa sai zazzaɓi ya rufe ni. Sai babata ta garzaya da ni asibiti. Muna zuwa sai aka yi mini allura, daga nan kuma sai na yi barci. Bayan da na farka sai babata ta kira ni domin na sha maganina, amma kuma sai na kasa tashi. To wannan shi ne farkon*

*samun wannan nakasa tawa.“*

**Mai ba da labari:**

Cutar da aka gano Lois ta kamu da ita dai ita ce cutar shan-inna, wato ‘polio’, wadda cuta ce mai yaɗuwa da haddasa shanyewar wani ɓangare na jiki. Tun daga wannan lokaci sai Lois ta zamo ba ta iya tafiya. Mahaifiyarta ta ci kuka kamar idonta zai fita. Mahaifinta kuma ya fusata da likitoci kuma ya yi ta la’antarsu. Shi a ganinsa laifinsu ne da ta kasa tafiya. Duk da haka sai ya sa Lois a makaranta. Bayan da ta kammala karatunta, kuma ta samu horon sanin makamar aiki, sai Lois ta samu wannan aiki da take yi yanzu. Yanzu dai wannan mata mai yawan fara’a tana cike da wani buri: so take a cikin wannan shekarar ta koma makaranta, ta karanci Harkokin Mulki. Abu guda dai da ya bayyana a tarihin wannan baiwar Allah shi ne, da ba don irin tallafin da iyayenta suka yi mata ba, da ba za ta taɓa kaiwa wannan matsayi da ta kai ba a yau. Baya ga ƙarfafa mata gwiwa da iyayenta da ’yan’uwanta suka yi, sun tabbatar da cewa ba a nuna mata bambanci ba. Akwai wani abu da ya faru da Lois ba za ta taɓa mantawa da shi ba.

**Bayanin Lois:**

*“Na tuno wata rana bayan mun dawo daga makaranta ni da ƙanina, sai wani yaro ya ce mini da Hausa, “Ke gurguwa!”. Da ƙanina ya ji haka sai ransa ya ɓaci. Sai ya bi yaron ya yi masa kashedi. Tun daga ran nan bai sake kirana da wannan suna ba.”*

**Mai ba da labari:**

Keken Lois dai shi kansa wata matsala ce mai zaman kanta. Duk lokacin da take tafiya da shi sai ya yi ta ƙara. Dole sai tana yi tana sa ƙarfi kafin ya tafi. A cikin ranta tana fatan samun keke mai aiki da wuta wanda zai dace da halin da take ciki. Amma kuma zai yi wuya a samu irin wannan a Najeriya. Ga dai Sergio Mainetti, shugaban wata ƙungiya mai suna ‘Christoffel-Blinden-Mission’ da ke Abuja, zai yi mana ƙarin bayani a kan dalilan da suka sa irin wannan keke ba ya samuwa.

**Bayanin Sergio:**

*“Duk irin kekunan guragun da muke da su a nan Najeriya kekuna ne ƙirar ƙasar Caina. Duk kantunan sayar da maganin da ka shiga za su ce maka akwai keken guragu, ba tare da sun tambaye ka irin halin da wanda za a saya wa keken yake ciki ba, ko kuma wane irin girman jiki ke gare shi ba, ko kuma muhallin da za a dinga amfani da keken.”*

**Mai ba da labari:**

Sai dai kuma duk da ƙwazon da Lois take da shi abu ɗaya yana nema ya gagareta: tana son ta haifi ’ya’ya, kuma tana burin samun mijin da ya dace da ita. Ita ma tana son a ce tana da nata iyalin. A ’yan shekaru da suka wuce ta ɗauka cewa komai ya daidaita, amma kuma sai abubuwa suka sukurkuce. Ga dai yadda ta tuno abin da ya faru.

**Bayanin Lois:**

*“Mun fara soyayya da wani saurayi kamar shekaru uku da suka wuce. Yana sona har ma kuma ya kai ni gidansu iyayensa suka gan ni. Amma kuma da muka isa can, sai labari ya sauya domin kuwa iyayensa korata suka yi daga gidan, wai a kan me zai kawo nakasasshiya a matsayin surukarsu. Sun nuna cewa sam haka ba za ta yiwu ba matuƙar suna raye.”*

**Mai ba da labari:**

Lois ta dage cewa ko me zai faru, sai ta nuna wa maza cewa abin fa ba yadda suka ɗauka yake ba.

**Bayanin Lois:**

*“Yawancin samari ganinmu suke a matsayin matan da ba za su iya kula da gida ba. Wasu ma gani suke ba za mu iya mu’amala irin ta auratayya ba. Amma kuma mu mun san za mu iya. Kuma iyawar ma ba ta wasa ba. Mu masu kula da gida ne. Ni a ganina ma mun fi kowa iya kula da shi.”*

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, idan dai kuna biye da mu, a yau mun gana ne da wata mata ce nakasasshiya mai suna Lois Auta daga Abujan Najeriya. Wadda ta kawo mana wannan rahoto dai ita ce Katrin Gänsler. Idan kuna son sanin wani abu game da irin kallon da ake yi wa mutane 'yan tsirarru a ƙasashen Afirka, sai ku saurari wannan shiri ta adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuna iya haɗewa da mu a muhawara a shafinmu na 'Facebook'. Muna fata kun ji daɗin shirin, mu huta lafiya.